# Takardar Aiki ta Gwajin Nau'ukan Sauyi da Abubuwan da ake so a kai gare su

## Wannan ƙungiya ta samar da taimako domin samar da samfuri na Ra'o'in Sauyi da za a iya amfani da shi a yayin da ake samar da ayyuka da tace su.

### Haɗawa Bibbiyu da Watsawa. Haɗa mutanen ƙungiya bibbiyu sannan su duba tambayoyin da ke biye:

- Me ke bukatar sauyi sannan wa? Duba waɗanda ke biye:
  - **Nau'ukan Sauyi** = Ɗabi'u, Halaye, Ma'aikatu
    Ra'o'i daban-daban na sauyi kan ƙarfafa nau'ukan sauyi daban-daban. Sashen Kulawa da Rage Rikici na USAID ya rarraba waɗannan nau'uka gida uku iyalai -Ɗabi'u, Halaye da Ma'aikatu. Waɗannan ba za su wanzu a lokaci ɗaya ba tun da ToC ɗaya na iya duba halaye da ɗabi'u ko halaye da ma'aikatu, ko ma ukun gabaɗaya.
    - **Iyali na 1: Garambawul a Ɗabi'u.** Wannan iyali na bukatar yin tasiri ga ɗabi'u da abubuwan da ke kawo natsuwar zuci da ma tasirin faɗakarwa mai yawa. An yi hasashen cewa sauyin ɗabi'u lamari ne mai ɗaukar lokaci, saboda ɗabi'u sun fi wahalar gyara fiye da halaye. Garambawul a kan ɗabi'u yana son kai wa ga mutane masu yawa amma yana iya kai wa ga muhimman mutane.
    - **Iyali na 2: Garambawul a Halaye.** Wannan iyali na hasashen cewa, za a iya sauya halaye kaitsaye, ba tare da neman sauyin ɗabi'a ba. Za a iya samun nasarar sauyin hali ta hanyar magancewa ko rage abubuwan da ke kawo rikici waɗanda ma'aikata da masu faɗakarwa za su yi, magance matsalolin tsaro daga ma'aikata, ko sauya tasirin ma'aikata a rikici – mayar da ayyukan da ke kai wa ga rikici masu tsada da mayar da waɗanda ke kai ga zaman lafiya masu sauƙin samu. Garambawul a halaye yana son kai wa ne ga muhimman mutane.
    - **Iyali na 3: Garambawul a Ma'aikatu** yana ƙarfafa sauye-sauye na tsari. Ma'aikatu masu tasiri, da suka haɗa da ma'aikatun shari'a da jin daɗin al'umma, za su iya taimaka wa wajen magance rikici, amma idan ba su aiki yadda ya dace ko aka samu baraka a tsakanin ma'aikatu, to rikici zai iya barkewa. Ma'aikatu kan mai da hankali ne ga hanyoyin samar da sauyi ga kokari da halaccin ma'aikatu domin bunƙasa tasirinsu.
  - **Waɗanda ake so Sauyi ya kai gare su** = Muhimman Ma'aikata, Masu Amfana na Kaikaice Kamar yadda aka samo daga takardar Tunanin CDA a kan Ayyukan Zaman Lafiya, waɗanda ake so sauyi ya kai gare su sun rabu azuzuwa biyu - Muhimman Mutane da Mutane Masu Yawa.
    - **Muhimman mutane:** Ɗaiɗaikun mutanen da suke da ƙarfi ko tasiri, kamar shugabannin ƙungiyoyi masu ɗauke da makamai, shugabannin gwamnati da na siyasa, shugabannin ƙabilu masu ƙarfi da shugabannin addinai, da sauransu. Waɗannan za su iya haɗawa da shugabannin ƙungiyoyin mata waɗanda ke da tasiri a rayuwar yau da kullum.
    - **Mutane masu yawa:** Al'ummomi, yawan mutanen da ake so sauyi ya kai gare su, ko mazauna yanki.

### Yi amfani da takardar aiki da ke ƙasa domin cika Waɗanda ake so Sauyi ya kai gare su da Nau'ukan Sauyi. Ba dole ne sai ka cika kowa gida ba.

- Kafin ku rubuta samfuri na Ra'in Sauyi, ku yi la'akari da: Ta yaya sauyin zai faru? Ta yaya hasashe ke tasiri a kan sauyin da kuke nema?
- Sai kowace haɗaka ta mutum biyu ta yi ToC. A tsarinsu mai sauƙi, an bayyana ra'o'in sauyi a matsayin zantuttukan "idan/sai"; "Idan muka yi X (aiki), sai mu samar da Y (sauyi/garambawul zuwa ga zaman lafiya, kwanciyar hankali, tsaro)." Kara hasashen da aka bayyana da kuma dubarar me ya sa muke tunanin X za ta samar da Y, ta hanyar kara Z – "saboda." A yayin da ra'o'in sauyi ba ta wannan hanyar ake rubuta su ba koyaushe, dukkansu suna bayyana wane sauyi ake tsammanin ya faru, yaya ake tsammanin ya faru, sannan me ya sa ake tsammanin ya faru.
- Kowace haɗakar bibbiyu za ta watsa ToC tare da babbar ƙungiya domin ganin wuraren da ke da zoba.
- Bayar da damar lokaci, ƙirƙirar rungumar ToC daga daiɗaikun ToC na kowa da kowa.

| Nau'ukan Sauyi | | Waɗanda ake so Sauyi ya kai gare su |
|---|---|---|
| Garambawul a Ɗabi'u | | |
| Garambawul a Halaye | | |
| Garambawul a Ma'aikatu | | |